## Muna dab da Karshen Duniya!

# Allah

## mai-tsarki zai kawo ranar shari'a akan rana ta 21 ga Mayu, shekara ta 2011.

---

Duniya tana tsoron ranar shari'a kuma ita ce ranar da Allah zai lalace duniya domin zunuban yan'adam. Lallai daidai duniya take game da yadda ta gaskanta cewa ranar shari'a tana zuwa. Littafi mai Tsarki ya samar mana da sakonai da suke daidai sosai game da wannan ranar.

Littafi mai Tsarki ne tsarkakan littafi da Allah mai tsarki, wanda kuwa shi ne mahallicin wannan kyakyawan duniyan ya rubuta. Littafi mai Tsarki, ba tare da wata tambaya ba, littafi ne da ya dade, wanda aka kamalla cikin kimanin shekaru 1,900 da suka wuce. Cikin asalin harsunan (wato yawancin suna daga Yahudanci da Helenanci ne), ba a taba canja ta ba, kuma kowane daya daga cikin kalaman, a cikin asalin harsunan daga bakin Allah suka fito. An raba Littafi mai Tsarki kashi biyu, zuwa (wato tsohuwar alkawari da sabuwar alkawari), sa'annan an raba kowane kashi zuwa littatafai da dama. Kowane littafi kuma an raba zuwa surori, sa'annan kowane sura an raraba zuwa ayoyi. Daya daga cikin littatafan an ace da shi littafin Timotawus ta biyu. Cikin sura ta 3, a aya ta 16 (wato Timotawus ta biyu sura 3 a aya ta 16) na wannan littafin, Allah mai-tsarki ya gaya mana cewa:

**"Kowane nassi hurarre daga wurin Allah mai-anfani ne ga koyarwa, ga tsautawa, ga kuwabewa, ga horo kuma da ke cikin adalci."**

Cikin Irmiya sura 36 a aya ta farko zuwa ta 4 Allah ya samar da wata misali na yadda aka rubuta Littafi mai Tsarki.

**"Ananan cikin shekara ta hudu ta Jehoiakim dan Josiah, sarkin Yahuda, wannan magana daga wurin Ubangiji ta zo ga Irmiya, cewa, ka dauki littafi, ka rubuta a ciki dukan magana da na fada maka a kan Israila, da Yahuda, da dukan al'ummai, tun ran da na yi maka magana, daga zamanin Josiah har yau. Watakila gidan Yahuda za su ji labarin dukan masifa da ni ke nufa in yi masu, har su juyo ga barin mugunyar hanyarsu dukansu, domin in gafarta masu muguntassu da zunubinsu. Sai Irmiya ya kira Baruk dan Neriah, Baruk kuwa ya rubuta dukan magana da Irmiya ya fada masa daga wurin Ubangiji a cikin littafin.** (Littafin na nufin Littafi mai Tsarki ke nan)**"**



Allah mai-tsarki ya ninka wa yadda zuciyan mu na yan'adam ke iya bayyanawa ko fahimtana. Cikin Farawa sura ta farko a aya ta farko Allah ya ce:

**"A cikin farko ya Allah hallici sama da kasa."**

Littafi mai Tsarki littafi ce da aka rubuta mana domin mu iya sani da cewa Allah mai tsarki ya hallici wannan kyakyawan duniya, kunshe da dukan itatuwa da dabbobi, da tsuntsaye, da halitatun abubuwa cikin ruwa, da kuma yan'adam wanda aka hallita domin su yi mulkin duniyan. Lallai babu wani hallita ta ko wacce iri da zai iya gwada kansa da Allah mai-tsarki. Ya gaya mana cikin Littafinsa mai Tsarki a cikin Farawa sura ta farko a aya ta 24 zuwa ta 26 cewa:

**"Allah kuwa ya ce, bari kasa ta fid da mai-rai kowane bisa ga irinsa, bisashe, da masu-rarrafe, da dabbobin duniya bisa ga irinsu. Haka kuwa ya zama. Allah kuwa ya yi dabbobi na duniya bisa ga irinsu, bisashe kuma bisa ga irinsu, da kowane abin da ke rarrafe a kasa bisa ga irinsa, Allah kuwa ya ga yana da kyau. Kuma Allah ya ce, bari mu yi mutum a cikin sifarmu, bisa ga kamaninmu. Su yi mulki kuma bisa kifaye na teku, da tsuntsaye na sama, da bisashe, da kuma bisa dukan duniya, da kowane abu mai rarrafe wanda ke rarrafe a bisa kasa."**

Mutanen da ke cikin duniya, wanda muna ce da su yan'adam, an hallice su ne domin su yi mulki akan wannan duniya. Allah ya bada dokokin wanda ta wurinsu zamu yi rayuwa da hikima da kuma farinciki har ya zuwa inda zai yiwu. Ya yi kashedu, ko da shi ke, cewa take wadannan dokokin zunubi ne, kuma zunubi zai kawo hukunci daga wurin Allah. Littafi mai Tsarki ya furta cikin Romawa sura 6 a aya ta 23 cewa "Gama, sakamakon zunubi mutuwa ne…".

Littafi mai Tsarki ya koyar da cewa Allah daya ne kadai akwai. Littafi mai Tsarki yace cikin Kubawar Shari'a sura 4 a aya ta 39:

**"ka sani fa yau, ka ajiye a cikin zuciyarka, Ubangiji shi ne Allah cikin sama daga birbis, bisa duniya kuma daga kalkas, babu waninsa."**

Domin Allah mai girma ne kuma cike da daukaka, sai yana kiran kansa da sunaye dabam-dabam. Kowane suna yana nuna mana wani sashi na daukar da kuma sifar Allah ne. Saboda haka, cikin Littafi mai Tsarki muna gamuwa da sunaye kamar su Allah, Jehovah, Almasihu, Yesu, Ubangiji, Allahu, Ruhu mai Tsarki, Mai-ceto da sauran su. Sunaye kamarsu Jehovah, Yesu, Almasihu mussaman suna nuna Allah ne a matsayin wanda kadai zai yiwo gafara daga dukan zunubai da kuma wanda zai samar da rai madawwami ta wurin ayyukan jinkan Allah masu daukaka. Domin Karin sakonai game da wannan batu, kana iya aika domin wannan littafi da ke kyauta, wato, "Ina fata Allah zai Cece Ni," wato *"I Hope God will Save Me,"* a turance.



An yi rubutun littatafai da dama game da Littafi mai Tsarki, ko kuma ana ganin su a matsayin kari akan Littafi mai Tsarki, kamar Kur'ani, ko kuma littafin Mormon. Amma ko da yaya dadewansu ko kuma kayatarwarsu, ko ma yadda aka karbe su a matsayin Littafi mai Tsarki ya ke, babu wani littafi ban da Littafi mai Tsarki da Allah ya rubuta da kansa, da kuma yake da tsarki kamar yadda Littafi mai Tsarki yake da tsarki. Allah ya yi kashedi cikin Ruya ta Yohanna sura 22 a aya ta 18:

**"Ina shaida wa kowane mutum wanda yake jin zantattuka na anabci na wannan littafi, idan kowa ya kara wa littafin nan, Allah zai kara masa anobai wadanda aka rubuta cikin wannan littafi."**

Kalmar nan "anoba" a cikin wannan aya yana magana ne akan hukuncin mutuwa da lalacewa da zai zo akan dukan wadanda sun aikata zunubi. Littafi mai Tsarki ya koyar da cewa, ko da shi ke, Allah yana kaunar wannan duniya, wanda shi cikin hikimarsa mara iyaka ya hallita, dokar Allah yana bidan hukuncin mutuwa akan wadanda suka yi zunubi. Littafi mai Tsarki ya ce a cikin Ezikiyel sura 18 a aya ta 20: "wanda ya yi zunubi, shi za ya mutu," sa'annan cikin Romawa sura 3 a aya ta 10 Littafi mai Tsarki ya furta da cewa: "babu mai-adalci (wanda bai taba zunubi ba), ko daya."

Dole Allah ya kiyaye dokokinsa shi ma, sa'annan, tun da dukan mutane na duniya sun zama masu zububi, dole zuwa karshe ya lalace duniya. A sarari ta ke cewa zunubi ya yi girma sosai a cikin duniya. Littafi mai Tsarki ya yi kashedi cikin Irmiya sura 25 a aya ta 33 cewa:

**"a ran nan fa za a ga kisassun Ubangiji tun daga wannan iyakar duniya zuwa wannan iyaka, ba za a yi makokin su ba, ba za a tattara, ba kuwa za a bizne su ba, za su zama taki a fuskar kasa."**

Ko da shi ke, Littafi mai Tsarki ya nuna mana cewa Alllah mai-tsarki Allah ne mai jinkai sosai, cike da tausayi da kuma kauna. Shi ya sa ya samar mana, tun kafin lalacewar, daidai lokacin ranar shari'a. Littafi mai Tsarki ya gaya mana cikin Amos sura 3 a aya ta 7 cewa:

**"Lallai Ubangiji Yahweh ba za ya yi kome ba, sai ya bayana asirinsa ga bayinsa annabawa."**

Saboda haka, yanzu muna iya sani daga Littafi mai Tsarki daidai lokacin da bayyanai da dama akan shirin Allah na lalacewa da ya ke zuwa akan dukan duniya.

Tun da sauran lokaci, muna iya kuka zuwa ga Allah da duk kaskanci domin jinkansa da alheransa. Watakila, tun da Allah mai jinkai ne, zai iya gafartawa wani wanda yake roka da duk kaskanci da Allah domin



jinkai. Allah ya yi alkawarai, alal misali cikin Zafaniya sura 2 aya ta 3:

**"Ku bidi Ubangiji, ku dukan masu-tawali'u na duniya, ku wadanda kuka kiyaye shari'arsa, ku bidi adalci, ku bidi tawali'u ko watakila za a boye ku a cikin ranar fushin Ubangiji."**

Allah mai-tsarki ya kwatanta mana da cewa yana iya lalace dukan duniyan nan domin zunubi. Littafi mai Tsarki ya samar mana da wannan gaskiyar mai-ban tsoro cikin Farawa sura 6 a aya ta 12 zuwa ta 13:

**"Allah ya duba duniya, ga ta kuwa, bataciya ce, gama dukan masu-rai sun bata tafarkinsu a duniya. Allah kuma ya ce wa Nuhu, matukar dukan abu mai-rai a gare ni ta yi, gama duniya cike ta ke da zalunci ta wurinsu, ga shi kuwa, zan hallaka su tare da duniya."**

Ta wurin nazarin Littafi mai Tsarki da kulawa sosai, mun koya cewa a shekara ta 4990 kafin zuwan Almasihu, Allah ya kawo ruwan tufana ya kuma lalace dukan duniya sai dai mutane takwas nan da kuma dabbobin da suke tare da su kadai. Ba a lalace su ba domin Allah ya kawo su cikin tsaron jirgin. Shugabansu, Nuhu, ya yi biyaya da dokar Allah na gina babbar kwale-kwale, wanda ana ce da ita jirgi, mai tsawon kafa 450 (wato mita 137).

Littafi mai Tsarki ya gaya mana cikin Ibraniyawa sura 11 a aya ta 7 cewa:

**"ta wurin bangaskiya Nuhu, da aka fadakar da shi a kan al'amuran da ba a gani ba tukana, domin tsoro mai-ibada, sai ya shirya jirgi domin ceton gidansa, ta wurin wannan fa ya kada duniya, ya zama magajin adalci wanda ke bisa ga bangaskiya."**

Kwanaki bakwai kafin ruwan tufana da ya rufe dukan duniya gaba daya ya fara, Allah ya dokace Nuhu ya fadakar da mutanen duniya da cewa suna da sauran kwanaki bakwai su shiga cikin tsaron jirgin. Littafi mai Tsarki ya gaya mana cewa akan rana ta bakwai ga watan biyu na wannan shekara ne Allah ya kulle kofar jirgin. Sa'annan, ruwan tufana ya soma domin ya gama rufe dukan duniya.

Kimanin shekaru 5,000 bayan wannan Allah ya rubuta a cikin littafinsa mai tsarki, a cikin Bitrus ta biyu sura 3 game da wannan lalacewar ta wurin ruwa da ta gama duniya a cikin kwanakin Nuhu. A cikin wannan surar ya sake fadakarwa da cewa lokaci na zuwa da Allah mai tsarki zai lalace dukan duniya da wuta. Dukan wannan duniya tamu za'a lalace ta har abada. Tsakanin wadannan furcin biyu na lalacewa mai gama duniya da zai zo sabili da zunubi, Allah ya yi wani magana mai muhimmanci. Allah ya ce cikin Bitrus ta biyu sura ta 3 a aya ta 8 da cewa:

**"Amma, kaunattatu, kada ku manta da wannan abu guda, rana daya a wurin Ubangiji kamar shekara dubu ce, shekara dubu kuma kamar rana daya ne."**

Allah ya rigaya ya rubuta a cikin Littafi mai Tsarki a Farawa sura 7 a aya ta 4 cewa:

**"Gama da sauran kwana bakwai, kana zan sa a yi ruwa a duniya yini arba'in da dare abra'in, kowane abu mai-rai da na yi kuma zan shafe shi daga dukan fuskar kasa."**

Allah ya kara da cewa a cikin Farawa sura 7 a aya ta 10 zuwa ta 11 cewa:

**"Ananan bayan kwanan nan bakwai, sai ga ruwan tufana bisa duniya. A shekara ta dari shidda ta zamanin Nuhu, cikin wata na biyu, kan rana ta goma sha bakwai ga wata, a cikin ranan nan sai mabulbulan zurfafa suka kakkarye, sakatun sama kuma suka bubbude."**

Jirgin da Nuhu ya gina ita ce kadai ta kasance wurin tsaro daga lalacewar tufanan. Haka ma, alheran Allah da jinkansa ne kadai wurin tsaro daga lalacewa da ke zuwa a ranar shari'a.

Cikin Bitrus ta biyu sura 3 a aya ta 8, wanda aka yanke dazun nan, Allah mai tsarki yana tunashe mu da cewa rana daya yana kamar da shekaru dubu ne. Saboda haka, da wannan sahihiyar fahimi da ke cewa kwana bakwai nan da aka yi zance akai cikin Farawa sura 7 a aya ta 4 ana iya fahimta su akan shekaru 7,000, zamu koya cewa a lokacin da Allah ya ke gaya wa Nuhu cewa da sauran kwana bakwai a tsere wa wannan lalacewar mai-gama dukan duniya, yana gaya wa duniya ke nan da cewa da sauran daidai shekaru 7,000 (wato rana daya na kamar shekaru 1,000) ne a tsere wa fushin Allah da ke zuwa a lokacin da zai lalace duniya a ranar shari'a. Domin Allah mai tsarki mara-iyaka ya san kome, ya san karshen tun daga farko. Ya san yadda duniya zata cika da zunubi.

Shekaru 7,000 bayan shekara ta 4990 kafin zuwan Almasihu (wato shekarar tufana) ita ce shekara ta allip 2011 ta kalandar mu). Wato lissafin ke nan 4990 a hada da 2011 sa'annan a debe 1 = 7,000

(4990 + 2011 – 1 = 7,000)

*(dole a debe shekara daya yayinda muke hayewa daga addadin shekaru ne kafin zuwan Almasihu a tsohuwar alkawari zuwa allip-allip na sabuwar alkawari domin kalandar bata dauke da wata shekara akan ta sifili ba).*

Saboda haka, Allah mai Tsarki yana nuna mana ke nan ta wurin kalaman littafin Bitrus ta biyu sura 3 a aya ta 8 cewa yana so mu sani da cewa daidai shekaru7,000 bayan ya lalace duniya da ruwa a kwanakin Nuhu, yana da shirin lalace dukan duniya



har abada. *Domin dai shekara ta allip 2011 daidai take da shekaru 7,000 bayan shekara ta 4990 kafin zuwan Almasihu, lokacin da tufanan ya fara, Littafi mai Tsarki ya samar mana da asalin shaida da cewa shekara ta 2011 ne karshen duniyan nan a lokacin ranar shari'a, wanda da zata zo a rana ta karshe na ranar shari'a.*

Abin mamakin kuwa, rana ta 21 ga Mayu shekara ta 2011, ita ce rana ta goma sha bakwai ga watan biyu bisa ga kalandar Littafi mai Tsarki na kwanakinmu. Tuna da cewa, ruwan tufana ya soma ne akan rana ta goma sha bakwai ga watan biyu a cikin shekara ta 4990 kafin zuwan Almasihu.

Littafi mai Tsarki ya samar mana da Karin shaidu masu ban mamaki da suke cewa ranar 21 ga Mayu shekara ta 2011 lallai daidai ta ke a matsayin lokacin ranar shari'a. Domin Karin sakonai akan wannan batu, kana iya aika domin wannan littafin da ke kyauta, "Muna Dab da Can" wato *"We Are Almost There,"* a turance, anan samunta kyauta daga Family Radio.

Allah yana tabbatar mana da cewa mun fa koya daidai daga Littafi mai Tsarki shirin Allah game da lokaci domin karshen duniya.

**BABBAN JINKAN ALLAH DA RAHAMARSA**.

Allah a cikin littafinsa mai tsarki ya bamu kyakyawan misali na rahamar jinkansa. Hade kuma a cikin Littafi mai Tsarki akwai littafin Yunana. A cikinta Allah ya yi magana akan wuta muguwar birni da ta kasance da mutane fiye da 120,000 da suka yi rayuwa kimanin shekaru 2,800 da suka wuce. An ce da ita Ninevah, wanda ta kasance babban birnin kasar Assyria ne da kuma basu san kome ba game da Littafi mai Tsarki. Amma domin muguntar su da kuma domin Allah mai Tsarki mai jinkai ne, ya aike wani annabi da ake da shi Yunana zuwa wannan birnin. Sakon Yunana daga wurin Allah zuwa gare su ita ce da cewa cikin kwana arba'in za a kabantar da dukan birnin.

Dukan birnin kuwa sun yarda da wannan daidai da dukan zuciyansu da cewa wannan fadakarwar fa daga wurin Aallah mai Tsarki ne. Saboda haka, daga sarkin har kasa zuwa ga bawa mafi karamci, sun tuba, wanda yana nufi da cewa sun juya daga zunubansu da girman kansu. Littafi mai Tsarki ya gaya mana da cewa sun sanya tsummoki sun zauna cikin toka. Wannan na nufi cewa lallai sun gane da cewa saboda zunubansu sun kunyatadda Allah. Sanya tsummoki a kuma zauna cikin toka wata aiki ne mai nuna kaskanci domin a nuna wa Allah a sarari da kuma dukan mutane nisan kaskanci da aka yi masu akan zunubansu ga Allah mai tsarki. Ya nuna cewa sun fa san da cewa sun cancanta Allah ya lalace su domin zunubansu.

Amma watakila, akwai begen cewa Allah na iya canja zuciyansa sa'annan a maimakon wannan ya yi jinkansu. Littafi mai Tsarki ya gaya mana cikin Yunana sura ta 3 a aya ta 6 zuwa ta 9 cewa:



**"Labarin ya kai har wurin Sarkin Ninevah, shi kuwa ya tashi daga kursiyinsa, ya tube alkyabansa, ya rufe jikinsa da tsummoki, ya zauna cikin toka. Ya sa aka yi shela, aka labarta ko'ina cikin Ninevah bisa ga umurnin sarki da hakimansa, cewa kada, mutum ko dabba, ko garken shanu, ko na tumaki su dandana kome, kada su yi kiwo, kada su sha ruwa kuma, amma su rufu da tsummoki, mutum duk da dabba, su tada muryarsu da anniya ga Allah, i, kowane dayansu shi juya ga barin mugun tafarkinsa, da zilama da ke cikin hannuwansa. Wa ya sani ko Allah za ya juya, ya tuba, ya bar zafin fushinsa, kada mu lalace?"**

Da ganin matukar kaskancinsu sai mun karanta game da jinkai Allah mai ban mamaki, fiye da ganewa kuma zuwa ga wadannan mugayen mutanen. Allah ya gaya mana cikin Yunana sura 3 a aya ta 10 cewa:

**"Allah kuwa ya ga ayyukansu, da suka juya ga barin mugun tafarkinsu, Allah kuwa ya tuba ga barin masifar da ya ce za ya yi masu, ba ya kuwa aikata ba."**

Domin dukan wannan muguwar birnin na Ninevah ta juya gaba daya daga mugayen tafarkunta da kuma matukar kaskanci sun yi kuka zuwa gun Allah domin jinkai, sai Allah mai Tsarki ya canja zuciyarsa sa'annan bai lalace su kuma ba.

Amma abin takaici, Littafi mai Tsarki ya nuna mana da cewa kima ne kawai daga cikin mutanen duniya ayau zasu juya daga mugayen tafarkunsu, da kuma matukar kaskanci da tsoro zasu yi kuka zuwa ga Allah domin jinkai. Ko da shi ke dai, Littafi mai Tsarki ya tabbatar mana da cewa da dama daga cikin mutanen da sun nema jinkan Allah baza a lalace su ba. Mun koya daga Littafi mai Tsarki da cewa Allah mai Tsarki yana da shirin kubutar da kimanin mutane milliyan 200 (wato kashi uku bisa dari ke nan na yawan mutane ayau). A rana ta farko na ranar shari'a (wato 21 ga Mayu, 2011) za'a chabke su (wato za a fyaucesu) zuwa cikin sama domin Allah ya yi masu jinkai babba. Wannan ya sa mun zama da godiya sosai zuwa ga Allah domin ya sanar mana da ranar shari'a da wuri. Domin Allah mai jinkai ne sosai, watakila ya yi maka jinkai. Littafi mai Tsarki ya ce a cikin Zabura ta 51 a aya ta 17 cewa:

**"Hadayu na Allah karyayen ruhu ne, karyayar zuciya mai-tuba ba za ka rena ta ba, ya Allah."**

Sa'annan cikin Zabura ta 51 a aya ta farko zuwa ta 3 Allah mai Tsarki ya nuna mana halin da ya kamata muna dauke da ita yayin da muke addu'a domin jinkansa:

**"Ka yi mani jinkai, ya Allah, bisa ga rahamarka, bisa ga yawan jiyejiyenkanka ka shafe laifofina. Ka wanke ni sarai daga kuskure na, ka tsarkake ni daga zunubi na. Gama ina sane da laifofina; zunubina yana gabana kullum."**

Abin takaicin kuma ita ce, ba za ka iya juya zuwa addinin ka, ko ka tafi wurin firsit naka ko fastonka, ko shugabanka cikin ruhaniya domin taimako ba. Suma ya kamata suna rokon jinkai Allah domin kansu. Wannan batu ne tsakanin ka kadai da Allah mai Tsarki. Allah ya san kowane tunaninka, kalaman ka da ayyukanka. Ka juya daga zunubanka sa'annan ka roka da duk kaskanci, ka bidi, ka kuma nema gafarar Allah.

Sa'annan, ka gode wa Allah da cewa cikin babbar jinkansa ya samar maka da wannan fadakarwan da ke cewa muna dab da lalacewa, da kuma babban begen da kaima, kana iya zama mutum da Allah zai kawo cikin sama domin ka kasance da Allah har abada cikin murna da farinciki da daukaka mafi kyau. Allah mai Tsarki a cikin Littafi mai Tsarki ya koyar da mu cikin Luka sura 18 a aya ta 10 zuwa ta 14 cewa:

**"Ya ce, mutum biyu suka tafi cikin haikali garin yin addu'a, daya Ba-farisi ne, daya kuma mai-karban haraji. Shi Ba-farisin ya tsaya yana addu'a da kansa haka, ya Allah, na gode maka ba kamar sauran mutane ni ke ba, azalumai, marasa-adalci, mazinata, ko irin wannan mai karban haraji. Lahadi daya ni kan yi azumi biyu, ina bada zakka daga cikin dukan abin da na samu. Amma shi mai-karban haraji, da ya ke tsaye daga nesa, ba ya yarda ya tada ko idanunsa sama ba, amma sai ya bugi kirjinsa, ya ce, Allah, ka yi mani jinkai, ni mai zunubin. Ina ce maku, wannan mutum ya tafi gidansa baratace ne bisa ga wancan, gama dukan wanda ya daukaka kansa za shi kaskanta, amma wanda ya kaskantadda kansa za shi daukaka."**

Bari Ubangiji ya yi maka jinkai kamar yadda ya yi wa wannan mai-karban harajin.

---

Domin Karin koyi game da bayyanan karshen duniya, ana gayatanka da cewa ka rubuta zuwa ga Family Radio, Oakland, California, 94621, USA kana neman a aika maka da wadannan littatafan da suke kyauta, ko kuma kana iya dubansu akan addareshin mu akan yanar gizo, www.familyradio.com.

• **"Ina Fata Allah zai Cece Ni"** wato **"I Hope God will Save Me,"**

• **"Muna Dab da Can,"** wato **"We Are Almost There,"**

• **"Daukaka Ya Tabbata ga Allah,"** wato **"To God be the Glory."**

Da wannan mun kamalla karatun mu na wannan karamar littafin. Allah ya sa ka mayar da hankalinka ga abubuwan da Allah zai sa ka yi da rayuwarka cikin karamar lokacin nan da ya yi saura wa duniya nan, duban abin da ka ji yanzu.



*HAUSA JD 06-29-10*